


 

Hikima da arziki da abinci abokan juna ne.
Wata rana sun yi tafiya mai nisa.
Sun shiga wani gari neman masauki.

?


  

Suna son su zauna a gida ɗaya.
Amma akwai tambaya da suke yi wa maigida.
Suna tambayar maigidan wane ɗayan su yake so.




Sun shiga gida na fari.
Sun ce sunayensu hikima da arziki da abinci.
Sun tambayi maigadi wa yake so a cikinsu.





Maigida na fari ya zaɓi arziki.
Arziki ya ƙi ya zauna a gidan.
Arziki ba zai daɗe ba in ba hikima.



Sun shiga gida na biyu.
Sun ce sunayensu hikima da arziki da abinci.
Sun tambayi maigadi wa yake so a cikinsu.



Maigida na biyu ya zaɓi abinci.
Abinci ya ƙi ya zauna a gidan.
Abinci ba zai daɗe ba in ba hikima.



Sun shiga gida na uku.
Sun ce sunayensu hikima da arziki da abinci.
Sun tambayi maigadi wa yake so a cikinsu.

Maigida na uku ya zaɓi
hikima.
Arziki yace shi ma zai
zauna a gidan.
Abinci ma yace zai zauna a
gidan.